TSATSUBA
Littafi Na Tara (9)
Part A
.
Marubucin Littafin
Abdul azis Sani M/Gini
Abubakar Saleh AlQuyraemey
.
Lokacin da dakarun sarki shardas suka fice daga cikin falon gasar domin cika umarnin da yayi musu na zuwa bayan gari su dauko masa matar attajiri amsar bayan sun kashe dakarun dake tsaron lafiyarta. Kawai sai sarki shardas ya tsugunna a gaban attajiri amsar wanda har a sannan bai daina kakarin mutuwa ba ya tallafo keyarsa da hannu guda ya dubeshi yace ta yaya kake tsammanin cewa zan barka ka rayu alhalin kafi ni kudi kuma kana da kyakkyawar matar da bani da kamarta kuma kana da karfin sihirin tsafi na ban mamaki ta yaya zan barka ka lashe wannan gagarumar gasa ka barni da abin kunya ?
.
To ka sani cewa komai sammakonka wani a tafe ya kwana, tun daga lokacin da akayi shelar wannan gasa nasa bokana ya shiga bincike akan sirrinka, don haka da gayya na gayyaceka izuwa wannan gasa domin naga bayanka sai a jiya ne bokan nawa ya gano cewa gaba daya tasirin sihirinka na tsafi yana jikin kwagirin da kake rikewa a hannunka in ba don na fisgeshi daga hannunka ba da ba zan taba iya kashe ka ba kaga kenan yanzu mutuwa zaka yi na gaje duk dukiyar nan da ka zo da ita kuma na gaji wannan kyakkyawar mata taka, Bani da wani buri a doron kasa wanda ya fi na ajiye tarihin da babu wani sarki ko wani boka ko jarumin da ya ajiyeshi, gama fadin hakan keda wuya sai attajiri amsar ya yunkura cikin karfin hali ya cakumi kwalar rigar sarki shardas ya budi baki da kyar cikin murmushin karfin hali yace tabbas ka sami nasarar hallakani to amma ka sani matata tana da kariyar dani kaina bani da ita don haka ina tabbatar maka da cewar har abada bazaka mallaketa ba sannan kuma matata tana dauke da juna biyu tsawon wata biyar duk abinda ta haifa namiji ko mace sune zasu dauki fansar raina a hannunka bakin azzalumi.
.
Koda gama fadin hakan sai idanun Attajiri amsar suka kafe gaba dayan jikinsa ya sandare ya zama gawa koda ganin haka sai sarki shardas ya kurma uban ihu wanda ya razana kowa dake cikin dakin gasar kawai sai ya zare takobinsa ya dubi wazirinsa ya damka masa kubar gidan darul daulat yace kowa ya fita ka kullue mini gidana, yanzu zan tafi izuwa can bayan gari na gani ko dakaruna sun cika aikinsu yana gama fadin hakan ya juya ya cife daga cikin gidan da gudu ya shiga jirgin ruwa aka ketare kogin dashi yana isa bakin gabar kogin ya fito daga cikin jirgin ruwan ya sake hawa doki ya zabureshi da gudu ya nufi hanyar bayan gari da karfin sihirin tsafi sarki shardas ya shafe tafiyar kwana uku a cikin yini guda kacal amma kuma yana isa inda su matar attajiri amsar suka yada sansani bai iske komai ba sai gawarwakin dakarunsa dana attajiri amsar gaba dayansu babu wanda ya tsira da rayuwarsa, ga keken dokin da matar attajiri amsar ke ciki amma babu ita babu alamarta, nan fa sarki shardas ya dimauce kuma ya haukace yayi ta neman mahaifiyata a cikin daji yana ihu yana kwallah mata kira amma shiru kamar maye yaci shirwa bisa dole ya hakura ya juya ya koma birninsa cikin tsananin bakin ciki da takaici.

.
Lokacin da yarinya Rulaiya tazo dai dai nan a labarinda take baiwa yarima hulkas sai tayi shiru ga barin zancenta a lokacin da hawaye ya zubo mata, cikin kaduwa da zumudi yarima hulkas ya dubeta yace to daga nan kuma menene ya faru ga mahaifiyarki shin guduwa tayi sa adda dakarun sarki shardas suka kawo musu hari, koda jin wannan tambaya sai yarinya rulaiya tasa hannu ta share hawayanta sannan tace mahaifiyata
ba gudu tayi ba ta bani labarin cewa agaban idanunka aka fafata KAZAMIN YAKI tsakanin dakarun sarki shardas dana mijinta masu tsaron lafiyarta kuma gaba dayansu sai suka yi RAGAS Faruwar hakan keda wuya sai taji jiri ya fara dibarta daga can kuma sai ta yanke jiki ta fadi kasa sumammiya lokacin da mahaifiyata ta farfado daga suman da tayi ne sai ta tsinci kanta a cikin wannan gida kwance a kas a gaban wani Aljani ma abocin kwarjini da ko a labari bata taba jin kamarsa ba.
.
Ba tare da aljanin ya gabatar da kansa a gareta ba ya dubeta a lokacin da gaba dayan jikinta yake karkarwa saboda firgita da ganinsa yace ki kwantar da hankalinki ya ke matar sarkin attajiran duniya kiyi sani cewa babu mai cutar dake anan iya tsawon rayuwarki, domin na daukarwa mijinki wannan alkawari anan ne kadai zaki iya tsira daga sharrin abokan gabar mijinki irin sarki shardas.
.
Koda jin wannan batu sai zuciyar mahaifiyata ta buga da karfi ta dafe kirjinta da hannayanta biyu sannan ta dubi aljanin tace ina labarin masoyina amsar shin an gama wannan ga sa ne ta siyan gidan darul daulat ? Maimakon aljanin ya bata amsar wannan tambaya sai yayi nuni da hannunsa izuwa ga jikin bango take hoton duk abinda ya faru a dakin gasar ya bayyana tun daga ranar farko har izuwa zagaye na karshen gasar.
.
Koda mahaifiyata taga sarki shardas ya kashe mijinta sai ta kwalla uban ihu ta sake sulalewa kasa sumammiya wannan shine asalin sanadin da ya sa mahaifiyata ta kamu da cutar ciwon zuciya kuma ciwon ne ya zamo.sanadin ajalinta bayan haihuwata da shekara shida. Bayan mutuwarta ne wannan aljani ya cigaba da kula da ni kuma ya zamana cewa kullum yana koya mini yaki yana mai cewa nan gaba zan dauki fansa akan makiyina sarki shardas da ya kashe min mahaifina amma ba ba sai idan lokacin yayi, lokacin da ban sani ba ke nan har kawo i yanzu gashi gaba dayan rayuwata ta kasance a cikin kadaici in ban da uwata da kuma wannan aljani da ya cigaba da kula dani
kaine mahaluki na uku da na gani a gaba dayan fadin wannan duniyar, koda yarinya rulaiya tazo nan a labarinta sai ta fashe da matsanancin kuka,
.
Al amarin da ya sa yarima hulkas yaji ya kamu da tsananin tausayinta kenan gami da matukar kaunarta fiye da ko yaushe, don haka bai san sa adda shima idanunsa suka kama zubar da hawaye ba, tsawon yan dakiku dayansu baice uffan ba daga can sai ya dubeta cikin nutsuwa yace yake rulaiya ai labarina da naki duk kusan iri daya ne kuma abokin gabarmu guda ne, nan take yarima hulkas ya zaiyane mata tun daga farko har karshe da yadda akayi ma ya tsinci kansa a wannan gida nata da kuma shirin da suke yi na tafiya neman hular lamsara don daukar fansa akan sarki shardas.

.
koda rulaiya taji wannan labari sai ta kamu da tsananin Al'ajabi sannan tayi shiru tana tunani da nazari daga can sai ta dago kai ta dubi yarima hulkas tace duk yadda akayi aljanin da ya ceci rayuwar mahaifiyata ya kawota nan kuma ya koya mini yaki shine ya daukoka ya kawoka nan lallai akwai wata manufa a cikin hadamu da yayi tunda duk burinmu iri guda ne, kash !
.
Zanso ace nima zanga yadda karshen gasar fadan yar uwarka jaruma siyama zai kasance da sadauki Darkus kuma zanso ace tare dani za ayi wannan gagarumar tafiya ta neman HULAR LAMSARA.
.
Kafin Rulaiya ta gama rufe bakinta sai kawai sukaga aljani Arwasul masadul ya bayyana tsuluum ! A gabansu yana mai kyalkyala dariyar farin ciki kawai sai ya dubesu duk su biyun cikin murmushi yace tabbas na gama cika aikina yanzu zan doraku akan tafarki na karshe wanda zaku dauki fansa kamar yadda na yiwa iyayenku alkawari daga nan zaku tafi izuwa can birnin sarki hulbasu tare kuma gobene za ayi wannan gasar ta karshe ke rulaiya ki boye fuskarki ga kowa kuma ki zamo mai taimakon su hulkas bisa duk abinda yazo musu zan baku wani tsuntsu wanda zai yi muku jagora izuwa inda hular lamsara take
ku sani cewa yanzu haka makiyanku sarki shardas tare da bokansa basu da burin da yafi su hadu dani domin na sanar dasu inda hular lamsara take amma wannan damar tuni ta wucesu ina mai gargadinku da ku kula sosai da wannan tsuntsu
da zan hadaku dashi domin ko yaya ku kayi sakaci ya subuce muku to fa zai koma hannun su sarki shardas ne ya kai su izuwa inda hular Lamsara take idan kuwa sarki shardas ya rigaku taba hular lamsara to dayanku ba zai tsira da rayuwarsa ba bare ma ya dauki fansa akansa.
.
Koda gama fadin wannan jawabi sai Aljani Arwasul masadul ya bude tafin hannunsa ya lumshe idanunsa yana mai karanta wadansu dalasiman tsafi faruwar hakan keda wuya ai ga wani farin tsuntsu dan karami wanda baifi girman kanari ba ya baiyana akan tafin hannun nasa gwanin ban sha awa, kawai sai ya mikawa yarima hulkas tsuntsun yace kaine ka cancanci rike wannan tsuntsu saboda kai kadai ne ka haye jarrabawata a duniya kai yakamata ka mallaki hular lamsara amma zanyi maka gargadi guda daya Gargadin kuwa shine duk abinda zaka so to ka soshi SAISA SAISA idan kuwa ka zurma a  cikin soyayyarsa tabbas  wannan abu shine Ajalinka, da wannan furuci nake yi muku bankwana na karshe har abada ba zamu sake haduwa daku ba ina mai yi muku fatan samun nasara akan babban makiyinku amma fa ku sani cewa aikin dake gabanku ya wuce yadda duk kuke zatonsa dole ne ku fuskanci BARAK WUYA da hadarurrukan da ba lallai ba ku kaiga gaci.
.
Aljani Arwasul Masadul na gama fadin hakan sai ya bace bat ! Tamkar bai taba wanzuwa ba a wajan, cikin rudewa yarima hulkas ya dubi yarinya Rulaiya yace saboda me wannan aljani zai tafi ya barmu ba tare da ya gaya mana yadda zamu iya kai kanmu can birnin sarki hulbasu ba da kuma yadda yakamata mu tafiyar da komai a cikin wannan gagarumar tafiya dake gabanmu.
.
Koda jin wannan batu sai rulaiya tayi murmushi sannan tace lallai kai so kake ma ka sami komai kenan a bati ?

To ka sani cewa ba a zama wane a banza kuma sai ansha bakar
wuya sannan ake shan dadi barina kimtsa sannan mu tafi ka jirani anan kada kayi karambanin zuwa ko ina ko taba wani abu a cikin dakin nan muddin bana kusa Rulaiya na gama fadin haka sai ta juya ta nufi cikin wani daki ta shige cikinsa ta rufe kofa.

.

Shi kuwa yarima hulkas sai ya kara kamuwa da tsananin mamaki yace a cikin ransa ' to wai shin menene a cikin wannan gidan mai hadari wanda har rulaiya zata gargadeni da kada in Tabashi ?

.

Ai kuwa matsoraci baya zama gwani don haka bari na yawata a cikin gidan nan na morewa idanuna kallo Gama ayyana hakan keda wuya sai yarima hulkas ya kama yawo a cikin gidan ya nufi
wani bangare daban yana kalle kalle yana mamakin irin yadda ginin gidan da kuma kayan alatun da aka zuba acikinsa nan take wani tunani ya fado masa a cikin zuciyarsa yace ni kuwa bayan mun sami nasarar kashe sarki shardas sai na shiga cikin gidan darul daulat na gani tsakaninsa da wannan gida nasu rulaiya wanne yafi girma da kawatuwa a cikinsa.

.

Koda yarima hulkas yazo nan a zancen zucinsa sai zuciyarsa ta buga da karfi tsoro ya kamashi ya tambayi kansa yace 'saboda me zan bar wa rulaiya wannan gida da dumbin dukiyar dake cikinta data kasance dukiya mai  tsananin yawa alhalin yane ranar farko dana fara ganinta a rayuwata shin wannan yana nufin ke nan na kamu da tsananin sonta fiye da yadda ma nake son iyayena da yar uwata siyama tunda gashi zan mallaka mata abinda su ban mallaka musu ba ai kuwa idan hakan ne maganar Aljani Arwasul masadul ce zata tabbata gaskiya, wato zan hallaka a dalilin soyayya kai ! Ba zai yuwu ba dole ne na takawa wannan soyayya birki komai zai faru gareni sai dai ya faru !!

.

Yarima hulkas na cikin yin wannan tunani ne yaga wata kofar daki ta bakin karfe wacce gaba dayanta a lullube take da yanah
a kura tamkar ma ba a taba bude ta ba, kawai sai yarima hulkas ya tunkari wannan kofa da zuwansa daf da ita ya sa hannu ya murda marukinta bisa mamaki sai yaga kofar ta bude ba tare da shakkar komai ba ya kunna kai cikin dakin koda yayi taku uku a cikin  dakin sai yaji kofar dakin ta kulle kanta cikin sauri ya koma da baya ya kama kofar da nufin ya bude amma sai kofar taki buduwa sai da yayi iya karfinsa har ya jike sharkaf da gumi amma ya kasa bude kofar.

.

Koda ganin haka sai ya saduda ya juya ya sake nausawa cikin dakin ba komai a cikin dakin face tarin gumaka na dakarun yaki
fululu babu adadi sai dai kowanne badakare yanayin shigarsa daban da dan uwansa kuma makamin yakinsa ma daban, gaba dayan wadannan dakarun yaki suna da siffa ta kwarjini da ban tsoro duk kuwa da cewa gumaka ne komai jarumtakar mutum da dakewar zuciyarsa sai ya firgita da ganinsu saboda gani zaiyi tamkar masu raine ba gumaka ba nan fa uarima hulkas ya cigaba da ratsawa ta tsakiyar gumakan dakarun domin ya isa karshensu, sai da ya yi yar doguwar tafiya sannan ya iso karshen dakim, nan take yayi arba da abinda yai matukar daure masa kai, ba komai ya gani ba face tarin dukiya mai tsananin yawa tsubi tsubi zube a kasa ta lu

u lu u zinare da yakutu wacce inda za a yi aikin kwasheta da magalar rakuma sai an shafe a kalla kwanaki dari ana dibarta bata kare ba.

.

Koda yarima hulkas ya dubi jikin bangon dake gaban wannan dukiya sai yaga anyi rubutu kamar Haka '- WANNAN DUKIYA HARAMTACCIYACE GA KOWANNE MAHALUKI, BABU WANDA YA ISA YA DAUKO KODA KWAYAR ZARRA A CIKINTA HAR YA FITA DA ITA DAGA CIKIN WANNAN DAKI !!

.

Sa adda yarima hulkas ya gama karanta wannan jawabi sai ya bushe da dariya yace ka ji wani zancen banza kuma ya ma za ayi ace wai ba zan iya daukar koda kwayar zinare daya ba alhalin babu mai gadin wannan dukiya a cikin wannan daki face wadannan gumakan banza ??

.

Gama fadin hakan ke da wuya sai yarima hulkas ya luma hannunsa a cikin tarin lu'u lu'un ya duntso cikin hannunsa ya zuba a cikin Aljihunsa, koda ya juyo da nufin ya koma da baya can inda kofar dakin take sai kawai yaga gaba dayan wadannan gumaka na dakarun yaki sun yi girgiza sun zama rayayyu suna karkade kurar jikinsu gami da zare makaman yakinsu kuma gaba dayansu sai suka durfafo inda yake.

.

Cikin firgita yarima hulkas ya daka tsalle bay a dai dai lokacin da daya daga cikin su ya kawo masa wawan sara da wani katon barandami, koda yarima hulkas ya goce barandamin ya sari wata dirkar gini mai kaurin gaske sai dirkar ta rabe gida biyu ta fadi kasa saboda karfin saran da kuma kaifin barandamin.

.

Al amarin da ya kara razana yarima hulkas kenan babu shiri ya zare takobinsa ya tari dakarun aka ruguntsume da AZABABBEN YAKI......

To nima dai AlQuyraemey ganin wannan azababben yakin da

ake fafatawa yasani dakatawa a wannan waje saboda haka sai kuma Allah ya kaimu wani lokacin sannan zan cigaba daga inda na tsaya.

TSATSUBA

Littafi Na Tara (9)

Part B.

.

Marubucin Littafin

Abdul azis Sani M/Gini

Abubakar Saleh AlQuyraemey

.

.

Al amarin Da ya kara razana yarima hulkas kenan babu shiri ya zare takobinsa ya tari dakarun aka ruguntsume da azababben yaki, hakika masu iya magana sunyi gaskiya da sukace tsuntsun da yaja ruwa shi ruwa kan doka nan fa dakarun yakin suka kuntata yarima hulkas suka rinka kai masa SARA DA SUKA ta ko ina ya zamana cewa da kyar yake iya kare kansa idan ba don ma yana da zafin nama ba da tuni sunyi gunduwa gunduwa da sassan jikinsa, nan take ya

raina kansa nadama tazo masa bisa gangancin da yayi ya taba wannan dukiya alhalin an gargadeshi, cikin kankanin lokaci dakarun suka yiwa yarima hulkas rauni har guda biyar a jikinsa ya zamana cewa jini na zubar masa kuma jiri
ya fara dibarsa amma saboda jarumtaka da juriya da mugun naci yaki yarda yaje kasa, a haka ya cigaba da maida martanin sara da sukan da suke kawo masa yana kare miyagun hare harensu kokarinsa shine ya kutsa ta tsakiyarsu ya isa can inda kofar dakin take ya sake jarraba budeta amma sai abun ya gagara, Ana cikin wannan bakin gumurzu ne daya daga cikin dakarun ya shammaci yarima hulkas ya gabza masa wawan naushi a kasan habarsa saboda karfin naushin sai da yarima hulkas yayi sama ya gwaru da rufin dakin jini yayi feshi daaga cikin hancinsa da bakinsa ya fado kasa tIm magashiyan, ai kuwa sai dakarun suka yunkura da nufin su gididdibashi, kwatsam ! Sai suka ji an doki kofar dakin ta balle daga jikin garu ta fado kansu sama suna juyowa suka ga ashe Rulaiya ce ta dako tsalle sama izuwa tsakiyarsu tayi wata irin katantanwa ta tarwatsasu da saran takubban hannayanta biyu kafin su sake taso mata ta dira a gaban yarima hulkas wanda ke kwance magashiyan kawai sai ta kama kafarsa da hannu daya ta dagashi sama ta zazzage su, nan take duk lu'u lu un da yarima hulkas ya diba ya zuba a cikin Aljihunsa ya zubo kasa faruwar hakan keda wuya sai gaba dayan dakarun yakin suka kame suka koma gumakansu tamkar
basu taba motsawa ba.
.
A sannanne Rulaiya ta sunkuya ta dauki yarima hulkas ta sabashi a kafadarta ta fice daga cikin dakin ta kaishi can turakarta ta shiga dinke raunikan dake jikinsa cikin gaggawa don ceto rayuwarsa, jaruma rulaiya na cikin yiwa yarima hulkas dinkine a raunikansa kawai sai taga ya suma, bayan ta gama dinke raunikan sai ta shafa masa magani sannan ta koma gefe daya nesa kadan da kan gadon da ta shimfideshi ta zauna akan wata kujera ta kura masa idanu nan take taga ashe yarima hulkas kyakkyawane na gaske, abin kwatance kuma yana da kira sosai irin ta manyan sadaukai kawai sai taji zuciyarta tana mai ayyana mata cewa wannan shine irin namijin da yakamata ta aura nan gaba idan ta girma ta cika cikakkiyar ya mace, wata zuciyar kuma sai ta kwabeta ta ce da ita baki da hankaline? Ashe har kin manta da kashedin da Aljani Arwasul masadul yayi
miki cewar kada ki kuskura kiyi soyayya da wani da namiji a lokacin yarintarki face kin isa aure?
.
Koda gama aiyana hakan sai rulaiya ta mike tsaye da sauri ta fice daga cikin dakin, domin ta daina kallon fuskar yarima hulkas kada zuciyarta ta kamu da sonsa, yarima hulkas bai farka daga dogon suman da yayi ba sai kashe gari da sassafe. A firgice ya farka yana yin arba da rulaiya zaune a gabansa tana kalaci sai ya dubeta cikin tsananin farin ciki yace A wanne lokaci muke a yanzu Dare ne ko Safiya?
Shin mun makara wajen zuwa birnin sarki hulbasu domin ganin gasar karshe ta yar uwata.
.
Koda jin wannan tambaya sai rulaiya tayi tsaki tace ai idan ma muka makara kaine ka janyo ashe kunnenka na kashi ne ban sani ba me yasaka ka ki bin umarnina alhali na gargadeka akan ka tsaya a inda na barka kuma na gaya maka cewa kada ka taba komai a cikin gidan nan in ba don nayi gaggawar kawo maka dauki ba da tuni yanzu ka zama gawa koda rulaiya tazo nan a jawabinta sai yarima hulkas ya Yunkura da kyar cikin matukar karfin hali ya tashi zaune

daga kwancen da yake ya zuro kafafunsa daga kan gadon da nufin ya takesu amma sai ya ji ya kasa saboda raunikan dake kan cinyoyinsa nan take takaici ya kamashi har kwallah ta ciko a idanunsa ya dubi rulaiya cikin alamun karayar zuciya yace ina rokonki da ki gafarta mini bisa rashin bin umarninki kuma ina kara rokonki daki daukeni a haka cikin halin da nake ciki ki kaini birnin sarki hulbasu akan lokaci domin naga gasar nan ta karshe tsakanin yar uwata jaruma siyama da sadauki Darkus.

.

Koda jin wannan batu sai Rulaiya tayi tsaki tace amma dai kai wawa ne wato kai bama ka damu da lafiyarka ba kawai so kake na kaika kaje kayi kallon gumurzun wasa to ka sani cewa kai rago ne ba jarumi ba kuma baka iya komai ba a yaki. Ba zaka iya tsinana abin arziki ba a cikin gagarumar tafiyar dake gabanmu dole sai na baka horo mazaka dauko dan jagoranmu ka rikeshi a hannunka yanzu nan zamu tafi birnin sarki hulbasu kafin a fara wannan gasa ga jagoran namu can a bayanka, koda gama fadin haka sai rulaiya ta bude wata akwatu dake kusa da ita ta debo kayan yaki ta shiga yin damara, shi kuwa yarima hulkas sai ya waiga bayansa da sauri nan take yayi arba da Wannan tsuntsun sihiri wanda aljani Arwasul masdul ya bashi kawai sai ya bude tafin hannunsa shi kuwa tsuntsun sai ya taso a sama yana mai kada fuka fukansa ya dira akan hannunsa yana mai kura masa idanu cikin murna, cikin kankanin lokaci rulaiya ta gama yin gagarumin shigar yaki ta rataya tagwayen masu a gadon bayanta bayan ta sanya wani bakin sulke da bakaken takalmi dogaye iya kwaurinta sannan ta lullube kanta da fuskarta da bakin mayafi ya zamana cewa idanunta kadai ake gani a fili, koda gama wannan kimtsawa sai ta suri yarima hulkas daga kan gadon da yake kwance tamkar ta dauki buhun auduga ta goyashi a bayanta suka fice daga cikin gidan gaba daya, shi kuwa yarima hulkas sai ya damke tsuntsun sihirin a cikin tafin hannunsa guda yana mai matukar farin ciki bisa ganin cewa zasu tafi izuwa birnin sarki hulbasu wajan iyayensa da yar uwarsa, da fitowarsu kofar gidan sai yarima hulkas ya ga wani farin ingarman doki a tsaye shi kadai yana harbin iska tamkar aikoshi akayi garesu ba tare da jiran komai ba kuma ba tare da rulaiya ta dorawa dokin sirdi ba sai ta kama dokin ta haye bayansa tana goye da yarima hulkas din sannan tace dashi maza ka saki wannan tsuntsu dake hannunka shine zai nuna mana hanyar da zamu isa can inda kake so muje, koda jin haka

sai yarima hulkas yai sauri ya bude tafin hannunsa nan take wannan farin tsuntsu ya tashi sama ya bi gabas ai kuwa sai rulaiya ta zaburi dokin da gudu suka bi inda tsuntsun ya nufa nan fa yarima yaga dokin nasu yana yin wani irin matsanancin gudu na ban al ajabi tamkar tashi sama yayi domin karfin gudunsa yafi gaban kwatance, abin da yarima hulkas ya ayyana a ransa kawai shine wannan ba doki ba ne irin sauran dawakai kuma tabbas yayi imani shi wannan sihirtaccen dokine domin gani yake kamar dokin zai iya zagaye duniya gaba dayanta a cikin rabin sa a wannan shine abinda ya faru ga yarima hulkas bayan barci ya daukeshi a turakar yarima barmas kuma ya farka ya tsinci kansa a wani wuri daban mai ban Al'ajabi..

"  "  "

Al amarin sarki shardas da bokansa labarusa kuwa sai da suka kara shafe kwanaki tara cif a cikin daji suna farautar Aljani Arwasul masadul amma duk tsawon wadannan kwanaki basu sake haduwa da shi ba kuma ko duriyarsa basu gani ba. Al amarin da yai matukar fusata sarki

shardas kenan ainun bai san sa adda ya cakumi kwalar boka labarusa ba ya daka masa tsawa yace kai labarusa ! Nifa na gaji da wannan farauta ta jaki mai kaho ya zama dole a gareka ka gaggauta yin bincike a cikin hallarar tsafinka ka gano mana wata hanyar daban da zamu bi mu iya zuwa inda hular lamsara take cikin gaggawa.

.

Koda jin wannan batu sai boka labarusa ya fisge kwalar rigarsa daga hannun sarki shardas ya dubeshi yace ka kwantar da hankalinka ya shugabana idan ba don ance tsafi kogi bane da sai ince dakai bamu da wata mafita ko hanya da za a samu wadda zata kaimu ga mallakar hular lamsara cikin sauki da gaggawa to amma ba a koda yaushe kuma a kowanne irin yanayi a ko'ina komai na iya sauyawa lokacin da ba a zata ba, ba zan ki ta taka ba bari na duba mana na gani ko akwai wata mafitar bayan wannan gama fadin hakan keda wuya sai boka labarusa ya zauna a kas dirshan cikin rairayi sannan ya fiddo madubinsa na tsafi ya shiga karanta wadansu dalasimai na tsafi irin wadanda sarki shardas bai ma taba jin su ba, sai da boka labarusa ya dauki lokaci mai tsawo yana shafa madubin tsafin nasa idanunsa a rufe sannan ya tsaya cak, boka labarusa yace ya dodon sarakai ka yi sani cewa a cikin binciken nawa na gano mana wata hanya mafi sauki wacce zata kaimu ga isa kogon da aka ajiye hular lamsara cikin sauki da gaggawa amma sai dai akwai wata matsala babba  data bullo a cikin wannan lamari ka sani cewa yanzu a halin da ake ciki Aljanin da muke farauta ruwa a jallo aljani Arwasul masadul sun hadu da yarima hulkas harma ya bashi tsuntsun tsafi wanda zaiyi masa jagora izuwa inda hular lamsara take sannan kuma sai abu na biyu yarima hulkas ya hadu da wata babbar sabuwar abokiyar gabar taka mai suna Rulaiya wadda take da burin daukar fansa akanka kuma a yanzu haka ta goya yarima hulkas akan wani dokin sihirin tsafi da Aljani arwasul masadul ya hadasu dashi sun tafi izuwa birnin sarki hulbasu inda matarka shadila take bisa jagorancin wannan tsuntsun sihiri da Arwasul masadul ya bashi, na gano cewa akwai wani mugun shiri da ake yi maka a can birnin sarki hulbasu don haka lallai ina tabbatar maka da cewa sarki hulbasu yaci amanarka kuma yana son ya rabaka da matarka shadila a yaune za ayi gasar karshe ta jarumtaka a birnin nasa kuma a yau dinne ya shirya kashe gaba dayan dakarunka dake tsaron lafiyar gimbiya shadila, idan bamu je birnin ba akan lokaci zamu iske tuni ya gama dasu kuma yabi su yarima hulkas izuwa dauko hular lamsara.

.

Koda boka labarusa yazo dai dai nan a jawabinsa sai kan sarki shardas ya daure ya cika da tsananin mamaki da fargaba da kuma takaici, ya dubi boka labarusa cikin damuwa yace akan wanne dalili sarki hulbasu zaici amanata alhalin yana tsananin sona?
Shin wacece wannan sabuwar abokiyar gaba tawa wacce naji ka ambashi sunanta rulaiya wacce suke tare da yarima hulkas? .

.

Koda jin wadannan tambayoyi sai boka labarusa yace wannan sabuwar abokiyar gaba taka ba wata bace face Yar attajiri Amsar wanda ka kashe shi a cikin gidan darul daulat bayan yaci gasar da kukai ta siyen gida a karshe ka gaje dukiyarsa babban burin wannan yarinya rulaiya a duniya shine ta dauki fansar ran mahaifinta akanka kuma ta mallaki gidan darul daulat tunda mallakin mahaifinta ne Attajiri Amsar, haka shima a yanzu yarima hulkas bashi da wani buri wanda ya wuce ya hallaka ka don daukar fansar abinda ka yiwa ubansa hailur da dukkan zuriarsu ina mai sanar dakai cewa a halin yanzu tuni hailur da matarka gimbiya shadila sun

mayar da auransu a cikin birnin sarki hulbasu har sun tare a cikin wani kasaitaccen gida da sarki hulbasu ya basu.

.

Koda boka labarusa yazo dai dai nan a zancensa sai sarki shardas ya takarkare ya kwarara uban ihu irin wanda ke tarwatsa mazaje a filin fama komai jarumtakarsu da rashin tsoronsu. Kai inda ace akwai mace mai ciki a wajen da tuni ta kama nakudar dole saboda firgita da za tayi na jin wannan ihu na sarki shardas kananun jarumai da dakarun yaki kuwa firgicewa zasuyi su dimauta su kama sakin fitsari a wando, shi kansa boka labarusa wannan ihu na sarki shardas ya razanashi yasa zuciyarsa ta buga tsuntsaye da dabbobin dake cikin dajin kuwa gaba dayansu sai da suka kama guje guje da iface iface suna sauya sheka da shigewa cikin ramuka cikin matsanancin fishi sarki shardas ya dubi boka labarusa yace maza ka hanzarta kaini birnin sarki hulbasu kafin su yarima hulkas su isa can, cikin rawar jiki boka labarusa yayi tsafi wani katon Aljani ya bayyana tsulum a gabansa suka haye bayansa ya tashi dasu sama ya luluka izuwa cikin gajimare yana mai tsala azababben gudu tamkar tauraruwa mai wutsiya, Abinda sarki shardas bai sani ba shine shi kansa boka labarusan bashi da tabbacin zasu iya isa can birnin Na sarki hulbasu akan lokaci kafin komai ya gudana.

+¡ ++ ++

Acan birnin sarki hulbasu kuwa gari na wayewa aka tashi da tsananin tashin hankali a gidan sarautar saboda an nemi yarima
hulkas sama da kasa an rasa babu inda ba a duba ba acikin birnin ba har da cikin dazuzzuka amma kamar maye yaci shirwa ga shi kuma a can filin gasa jama a sun taru makil ana ta shewa da ihu ana jiran isowar sarki hulbasu da su jaruma siyama babu wanda yafi kowa tashin hankali sama da shadila domin tunda akace yarima hulkas ya bata take ta faman rusa kuka saboda gani take kamar ya fada hannun sarki shardas ne.

.

Da kyar hailu ya shawo kanta ya rarrasheta don kada ta tarwatsa musu dukkan shirinsu na ranar inda ya tabbatar mata da cewa yayi bincike a hallarar tsafinsa ya gano cewa yarima hulkas na nan a raye kuma zai dawo kafin a gama wannan gasa nan dai ya lallabata suka shiga cikin ayarin sarki hulbasu aka tafi filin gasa koda jama a suka jiyo bushin Algaita da bugun tambura alamar cewa sarki ya iso filin gasar sai filin ya sake rudewa da shewa gami da tafi nan fa aka bude kofar filin gasar sarki da mukarrabansa suka shigo bisa dawakai dakaru na take musu baya, amma abin da ya daurewa kowa kai shine sarki hulbasu yayi gagarumar shigar yaki tamkar yana cikin jaruman gasar haka ma dakarunsa na musamman masu tsaron lafiyarsa kuma a cikinsu har da wadansu bakin dakaru wadanda suka rufe fuskokinsu ba wasu bane wadannan bakin dakarun da ke bayan sarki hulbasu ba face su jarumi hailur.

.

Lokacin da dakarun sarki shardas masu tsaron lafiyar gimbiya shadila sukaga sarki hulbasu ya fito da wannan shiri sai suka sha jinin jikinsu suka fara zargin cewa lallai akwai wani abu dake shirin yi musu don haka sai suka fara yin kus kus a tsakaninsu, Abinda basu sani ba shine wanda duk ya rigaka kwana dole ne ya rigaka tashi kuma maso abinka yafika dabara, jaruma siyama na daga cikin tsakiyar dakarun sarki tayi gagarumar shigar yaki tare da mahaifiyarta bisa

doki guda,

.

Koda yan kallo suka ga siyama sai suka rude da ihu aka kama yi mata jinjina, ita dai kawai jaruma siyama tana yin murmushin karfin haline amma hankalinta a wannan rana a tashe yake saboda rashin ganin dan uwanta yarima hulkas.

.

Bayan sarki hulbasu da tawagarsa sun gama shigowa filin gasar kuma sun zauna a inda aka tanadar musu sai mai gabatarwa ya fara da kirawo sunan sadauki darkus nan fa magoya bayan darkus suka rude da shewa gami da tafi suka shiga yi masa kirari gami da jinjina koda aka bude wata kofa sadauki darkus ya fito yana tafiya kamar wani toron giwa a cikin gagarumar shigar yaki sai filin gasar ya yi tsit tamkar mutuwa ta gifta saboda kwarjininsu da karar sautin takun sawayensa har sai da sadauki darkus ya iso tsakiyar filin gasar ya tsaya mai gabatarwa ya kirawo sunan jaruma siyama sannan filin gasar ya sake kaurewa da shewa gami da yafi, cikin nutsuwa jaruma siyama ta fito daga cikin tawagar sarki hulbasu ta shiga filin gasar, har sai da ta isa.

.

Daf da sadauki darkus sannan ta ja ta tsaya a lokacin da tazarar dake tsakaninta da sadauki darkus bata wuce taku uku ba, ba tare da bata wani lokaci ba alkalan gasar suka bada umarnin a fara gasa nan take, aka buga tambarin fara gumurzu kamar hadin baki  sai duk su biyun a lokaci guda kowannansu ya juya da baya yayi taku bakwai sannan suka tsaya suka juyo suna masu zare takubbansu, kawai sai suka ruga da masifaffen gudun tsiya tamkar zasu tashi sama suna masu kwallah ihu mai firgitarwa suna jijjiga makamansu a sararin samaniya kafin su hadu sai kowannansu ya daka tsalle sama yakaiwa dan uwansa mummunan sara..
Kai nima AlQuyraemey ganin wannan saran ne yasa na tsaya a nan nace sai wani lokacin cewa sai Allah ya kaimu gobe.

Akwai littattafai guda Uku da nake aiki akansu nan bada jimawaba zan gama sune kamar haka:
1- Jarumin Jarumai
2- Gwarzon Sadauki
3- Jarumi Dan Baiwa wanda dukkansu Abdulaziz Sani Madakin Gini ne ya rubutasu ga mai so zai iya yi mani magana ta WhatsApp 08138873799

TSATSUBA
Littafi Na Tara (9)
Part C.
Marubucin Littafin
Abdul azis Sani M/Gini
Abubakar Saleh AlQuyraemey

.

Kafin su hadu sai kowannan su ya daka tsalle sama ya kaiwa dan uwansa mummunan sara, duka su biyun a tare suka duro kasa lokacin suna masu juyawa junansu baya, bisa mamaki sai aka ga kowannansu ya tsaya cak a inda yake ba tare da ya juyo ya cigaba da yaki ba, Al amarin

da ya baiwa kowa mamaki kenan a filin Gasar. Aka sake yin tsit a karo na biyu daga can kuma sai aka ga jaruma siyama da sadauki darkus sun waigo sun fuskanci juna shi yana mai dafe saman kirjinsa jini na zuba ita kuma tana mai dafa hakarkarinta Na hagu jini na zuba.

.

A sannan ne yan kallo suka gane cewa ashe kowannansu ya samu nasarar yiwa dan uwansa mugun rauni Cikin matukar juriya da jarumtaka sadauki darkus ya yagi rigarsa ya daure kirjin nasa tamau don tsaida jini itama jaruma siyama sai tayi sauri ta cire mayafin dake zagaye a wuyanta ta daure hakarkarin nata ba tare da jiran komai ba sai suka rugo izuwa kan juna suka kacame da masifaffen yaki mai matukar ban tsoro da ban al ajabi a wannan lokaci mahaifiyar siyama na zaune daf da hailur kuma tuni ta fara kuka bisa ganin yadda aka yiwa yarta rauni tun a farkon fara wannan gasa shikuwa hailur sai ya dubeta yace kwantar da hankalinki yake matata ni na san ko wacece yata ina mai tabbatar miki da cewa ba zata mutu ba kuma ita ce zata lashe wannan gasa sai da aka shafe sa auku cur ana wannan mummunan BAKIN ARTABU tsakanin sadauki darkus da jaruma siyama ya zamana cewa sun galabaitar da juna domin kowannan ya sami rauni kimanin guda biyu a jikinsa jiri ne ke dibarsu tamkar zasu sake yin RAGAS saboda karfi yazo daya ana cikin haka ne sadauki darkus ya shammaci jaruma siyama ya dankara mata wani karkarfan naushi a ciki saboda karfin naushin sai da jaruma siyama tayi sama da baya bayanta yaje ya gwaru da katangar filin gasar ta fado kasa da rub da ciki a matukar galabaice tana aman jini.

.

Koda sadauki darkus yaga ya sami wannan nasara sai ya bushe da dariyar mugunta ya daga takobinsa sama ya ruga izuwa inda
take ya daka tsalle sama da nufin ya duro kanta ya soke gadon bayanta tuni a wannan lokaci kowa ya gama sallamawa cewa jaruma siyama ta mutu ba zato ba tsammani sai aka ga jaruma siyama ta mirgina can gefe guda takobin sadauki darkus ta lume a cikin kasa kafin sadauki darkus ya zaro takobin tuni siyama ta doki kasa da tafin hannayanta biyu kawai sai gani akayi tayi sama kuma tayi katantanwa sannan ta doki kirjin sadauki darkus da kafafunta biyu, saboda karfin dukan sai da shima sadauki darkus yayi sama yaje ya gwara bayansa a jikin katangar filin gasar ya fado kasa a kan fuskarsa fuskar tasa ta dauje jini ya rufe masa idanu kafin a goge jinin dake kan idanun nasa tuni siyama ta daka sufa a sama izuwa inda takobinsa take ta zarota daga cikin kasa ta luma masa ita a ciki take takobin ta faso gadon bayansa sadauki darkus yayi mutuwar tsaye ya sandare kawai sai jaruma siyama tasa kafarta ta sake dukan kirjinsa sannan gawar tasa ta fadi kasa rikica kamar giwa ta fadi nan fa filin gasar ya rude da shewa gami da tafi ana yiwa jaruma siyama kirari bisa wannan gasa bayan ta kashe sadauki darkus a wannan lokaci ne kuma kwatsam sai aka ga jaruma siyama ta yanke jiki ta fadi kasa sumammiya.

.

A guje likitan sarki hulbasu da masu taimaka masa suka ruga zuwa filin gasar kan jaruma siyama don bata taimakon gaggawa
a dai dai wannan lokaci ne hailur yazo daf da kunnen sarki hulbasu yayi masa rada yace ya shugabana gada daya fa dakarun sarki shardas da suka rako shadila duk sun sulale sun gudu ga dukkan alamu sun gano shirinmu da jin wannan batu sai sarki hulbasu yayi murmushi yace ai nima tun dazu na lura da hakan amma ko kadan ban damu ba saboda na san cewa duk shirin da zasu yi a yanzu ba zai kai namu ba maza kaje ka karasa shirin komai ni da dakaru

zamu fara yin gaba saika taho da sauran iyalansu gama fadin hakan keda wuya sai aka ga wani karamin tsuntsu ya shigo filin gasar a sama bai dira a ko ina ba sai akan jaruma siyama wacce ke kwance magashiyan likita na yi mata magani tsuntsun na dira akanta sai aka ga ta bude idanunta ta rmike tsaye zumbur tamkar babu abinda ya sameta ta kurawa bakin kofar fita daga filin gasar idanu.

.

A dai dai wannan lokaci ne aka jiyo sukuwar doki ya nufo cikin filin gasar tashin kurane ya hana ganin dokin amma kurar na lafawa sai aka ga ashe wani farin ingarman doki ne dauke da mutum biyu na gaban dokin yarima hulkas ne na bayansa kuwa wani jarumi ne a cikin shigar bakake tufafi goye da tagwayen masu.

.

Koda jaruma siyama ta hango dan uwanta yarima hulkas bisa doki ya tunkarota sai fuskarta ta fadada da murmushi ta ruga gareshi da gudu. Nan take shima yarima hulkas ya duro daga kan dokin ya karasa gareta a guje suka rungume juna cikin tsananin farin ciki yana ma tayata murnar lashe wannan gasa a dai dai wannan lokaci ne yarima hulkas yaji an dafa kafadarsa ta baya yana waigawa yaga ashe sarki hulbasu ne shima ya rungumeshi cikin farin ciki sarki hulbasu yayi masa rada a kunne yace bamu da isashshen lokacin.

.

Lokacin yin wani bayani ga juna yanzu domin yin hakan zai sa mu bata lokaci yanzu mun gama shirin komai dama kai kadai muke jira maza ka dauko yar uwarka akan wannan doki naku duk da cewa ku uku ne ku sameni a bayan gari mahaifinka ma zai riskemu  a can nan take aka kawowa sarki hulbasu dokinsa ya hau dakarunsa suka take masa baya a lokacin da ya zaburi dokin nasa da gudu ya fice daga filin gasar.

.

Al amarin da ya daurewa yan kallo kai ke nan suka cika da tsananin mamakin dalilin da ya hana a tsaya a bayar da kyauta ga jarumar da ta lashe wannan jarumtakar da akayi wato jaruma siyama nan dai filin gasar ya waste mutane suka tafi suna hasashe da zargin cewa lallai babu lafiya yau.

.

Al amarin dakarun sarki shardas kuwa ashe gaba dayan suka sulale daga cikin filin gasar suka ruga izuwa cikin daji inda suka sake haduwa suka tattauna akan yadda za su sace gimbiya shadila cikin ruwan sanyi domin su mayar da ita gida kada fishin sarki shardas ya hau kansu nan take shugabansu sadauki Murzanu ya dubesu yace na yarda da jarumtakarku da nacinku gami da iya yakinku saboda haka yanzu zamu koma izuwa cikin wannan birni na askandariyya daya bayan daya kamar yadda muka hadu a nan yanzu kuma sai dare ya raba sannan zamu shiga har cikin gidan sarautar sarki hulbasu mu aiwatar da nufinmu.

.

A halin yanzu sarki hulbasu ya gaya mini cewa yanzu zai mana rakiya tare da gimbiya shadila da dakarunsa domin mu isa gida lafiya na nuna masa cewa na amince da hakan amma na san karya yake yi so yake ya shirya mana wani tuggun ya cutar damu
shi yasa nace mu rarrabu mu buya a cikin birnin nasa ba tare da ya sani ba tuni na aika da dakarun yan leken asiri domin su kai labarin abinda yake faruwa ga can birninmu saboda a sanar da sarki halin da muke ciki ta hanyar karfin sihiri a duk inda yake.

.
Koda sadauki murzanu yazo nan a zancensa sai ya sallami gaba dayan dakarun nasa suka rarrabu a cikin shiga ta bad da kama suka bi hanyoyi daban daban shi dai sadauki marzanu tare da wadansu dakarun nasa mutum dari biyu sai suka bi wata barauniyar hanya ta bayan wani katon tsauni sai da suka yi yar doguwar tafiya ta kusan tsawon dakika dari bakwai da arba in sai suka yi kicibis da sadauki Ruhaisu babban yaron hailur shima dakarunsa mutum dari biyu da goma na take masa baya, cikin tsananin kaduwa da mamaki sai sadauki marzanu suka tsaya cak suka dora hannayansu akan kufen takubbansu domin basu taba zaton cewa za a tarfasu ba haka, suma su sadauki ruhaisu sai suka dora hannayansu akan kufen takubban aka fara kallan - kallo, Take sadauki marzanu ya tuno da sadauki ruhaisu sa adda suka fafata kazamin yaki a can shekarun baya sa adda sarki shardas ya kaiwa kabilar su hailur hari suka karkashe su har sarki shardas yaje fa hailur kasan wannan tsauni mai tsawon gaske kuma ya dauke matarsa shadila ya tafi da ita shima ruhaisu ya gene sadauki marzanu sai zuciyarsa ta kama tafarfasa kamar zata kone saboda tsananin kiyayyar dake taso masa cikin tsananin fishi ya dubi sadauki marzanu yace yakai tsohon abokin gaba kayi sani cewa jama arku da sarkinku sun dasa mana bakin cikin da har abada ba zamu taba mantawa dashi ba amma na dade ina jiran wannan rana da takobina zata dau fansar jinin kabilata akanku na rantse da darajar shugaba hailur tsakaninmu daku dole ne wasu su zama gawa anan kafin
mu rabu.
.
Koda jin wannan batu sai sadauki marzanu ya bushe da dariyar mugunta yace kai samari hakika tsautsayi ne ya sa kuka yi wannan babban ganganci na tunanin taremu da yaki da kuma kokarin kwacewa sarki matarsa, ina mai tabbatar maka da cewa a wannan karon sai mun karar da ku gaba dayanku ta yadda har abada ba za a kara ganin irin zuri arku ba a doron kasa, koda sadauki marzanu yazo nan a zancensa sai sadauki ruhaisu ya tari numfashinsa yana mai daka masa tsawa yace kai wawa mara hankali da tunani shin ka manta ne cewa sarkin naku ne ya fara kwatar matar mu ?? Yanzu ne zamu dawo da abarmu garemu kuma mu dauki fansar jinin yan uwanmu da kuka salwantar ka sani cewa ku azzalumai ne masu cin zarafin talakawa sata kwace da danne hakki tsawon shekaru to ku sani cewa shi ramin karya kurarre ne kuma gaskiya.dokin karfe ce wanda baya taba mutuwa.
.
Koda gama fadin hakan sai sadauki ruhaisu ya zare takobinsa ya yiwa dakarunsa nuni da a afkawa abokan gaba, ai kuwa ba su tsawa jiran komai ba sai suka zare takubbansu cikin hanzari suma su sadauki marzanu suka zare nasu takubban aka ruguntsume da azababben yaki nan fa wuri ya hargitse kura ta tashi karar karafa da kururuwar mazaje ta fara cika kunnuwa.

-- -- --

Ragowarrdakarun murzanu kuwa su dubu daya da dari takwas sun sake rarrabuwa izuwa mutum dari hurhudu wannan shine babban kuskuren da suka tafka domin inda a cure suke gaba daya sai an kai ruwa rana kuma an kai gwauro an kai mari kafin a ci galaba a kansu.

++ ++ ++

Mutum dari hudu da suka nufi gabashin birnin askandariyya sai suka yi kicibis da tawagar sarki hulbasu nan ma sai aka kacame da Yaki amma da yake su sarki hulbasu sun ninkasu sau goma a yawa nan suka karkashesu a cikin kankanin lokaci basu bar daya ya tsira da rayuwarsa ba.

++ ++ ++

Dakarun da suka nufi yammacin birnin kuwa sai sukayi kicibis da yarima hulkas jaruma siyama da jaruma rulaiya bisa doki guda su uku, koda ganinsu sai yarima hulkas da siyama suka zare takubbansu da nufin su afka musu amma sai jaruma rulaiya ta dakatar dasu tana mai daga musu hannu har izuwa wannan lokaci rulaiya bata yarda koda jaruma siyama taga fuskarta ba domin a rufe take cikin bakin kyalle, take jaruma rulaiya ta duro kasa daga kan dokinta ta dubi dakarun nasu sadauki murzanu taga basu fi su dari hudu ba kawai sai tayi tsaki sannan ta juya ta dubi yarima hulkas tace ai abin kunya ne ace mu ukun nan ne zamu yaki wadannan kananan kwari kawai ku barni dasu rabin sa'a tayi min yawa na gama dasu.

.

Koda gama jin wannan batu sai dakarun sadauki marzanu suka fusata ainun suka zare takubbansu suka afkawa jaruma rulaiya gaba dayansu Wohoho Hakika mai karfi sai Allah ya isa kuma duk wanda ya iya ya huta ana fara wannan yaki sai jaruma siyama ta cika da tsananin mamaki bisa ganin irin jarumtakar jaruma rulaiya da kuma tsananin zafin namanta, domin duk yawan dakarun su dari hudu sai ya zama na banza saboda duk inda ta kutsa a cikinsu sai dai kaga maza na zubewa kasa domin gididdibasu ta rinka yi sassan jikinsu ya rinka zubewa yana faduwa kasa suna ihu kuma jini na feshi da fantsama.

.

Nan fa aka rasa mutum daya daga cikin dakarun wanda ya sami nasarar koda lakutar jikin jaruma rulaiya nan take jaruma siyama ta raina dukkan jarumtakarta ta fara tunanin cewa duk yadda akayi wannan hatsabibiyar bakuwar jaruma wacce yarima hulkas yazo da ita ba mutum bace Aljana ce.

.

Koda gama ayyana hakan a cikin zuciyarta sai ta kasa hakuri ta dubi yarima hulkas tace yakai dan uwana wai shin wacece wannan bakuwar jarumar da ka zo da ita kuma a ina ka sameta har yanzu ta fa ka bani labarin inda ka tafi ba muka nemeka muka rasa koda jin wannan tambaya sai jarimi hulkas yayi murmushi yace me yasa baki da hakuri ne yake yar uwata yanzu ina nake da lokacin baki labari a cikin wannan yanayi da muke ciki ki bari sai mun gama da wadannan abokan gaba namu tukunna mun isa can inda hular lamsara take in yaso bayan mun daukota mun kashe sarki shardas sai mu zauna na baku labari keda iyayenmu a cikin nutsuwa da kwanciyar hankali.

.

Koda jin haka sai jaruma siyama ta bata rai tace yama za ayi nayi ta hakurin jin wannan labari har sai mun kai ga wannan lokaci me ye tabbacinka ma cewa zamu tsira da rayukanmu har mu sami nasarar dauko hular lamsara har yarima hulkas yabudi baki zai ce da ita wani abu sai ya ga jaruma rulaiya ta daka tsalle sama ta kama yin wata irin katantanwa a sama tana fille

kawunan dakarun sarki shardas nan da nan ta karar da sauransu gaba daya ya zamana cewa babu dayansu da ya rage a raye saboda tsananin mamakin wannan gagarumar jarumtaka da jaruma rulaiya tayi yarima hulkas da siyama basu sansa adda suka wangame bakunansu ba suna kallonta.
.
Koda jaruma rulaiya ta dago kanta ta dubesu sa adda take goge jinin takobinta a jikin gawar abokan gabar da ta kashe taga ririn kallon da suke yi mata na al ajabi sai tayi murmushi ta dubi yarima hulkas tace kuzo mu yi sauri mu karasa gaba tunda bamu san halin da sauran yan uwanmu suke ciki ba ba tare da wani bata lokaci ba sai suka kara hawa kan wannan dokin sihiri na jaruma rulaiya su ukun suka zabureshi da gudu izuwa gaba saboda girman wannan doki da cikarsa duk su ukun sai da suka zamo yan kanana akansa.

++

Acan Inda yaki ya ruguntsume kuwa tsakanin su sadauki ruhaisu da su murzanu abin ya kazanta babu kyan gani saboda karfin yazo daya domin ragargazar kowanne bangare ake yi har ta kai cewa ana ta yin ragas sai da aka shafe sa a daya da rabi ana wannan mugun yaki har ya zamana cewa an karar da gaba dayan dakarun kowanne bangare saura mutum biyu kacal suna fafatawa, wato saura Sadauki Ruhaisu da Murzanu gashi dai kowannansu ya yiwa dan uwansa raunika har guda uku uku jini na zuba a jikinsu juwa na dibarsu amma saboda tsananin nacinsu da mugun buri na son ganin bayan juna kowannansu yaki yarda yaje kasa Lokacin da bala'i yakai bala'i ya zamana cewa sun gaji likis sai suka zube kasa bisa guiwoyinsu suna haki da numfarfashi kamar ransu zai fita bayan dan wani lokaci sai kowannan su ya mike tsaye da kyar sannan suka ja da baya taku bakwai bakwai tamkar sun hakura da yakar juna kwatsam kuma sai suka rugo da gudu izuwa kan juna suna masu kwalla ihu cikin mugun nufi duk wanda yaga lokacin da wadannan manyan jarumai suka tunkari junansu kasan cewa mugun gamo za ayi ko dai a mutu ko kuma ayiwa juna mugun lahani da zai iya zama sanadin Ajali, ai kuwa yana ragewa saura taku uku kacal su hadu sai kowannansu ya daka tsalle sama suka kaiwa junan su suka da takubbansu cikin sa'a kuwa kowannansu ya lumawa abokin
fadansa takobi a ciki ta faso ta gadon bayansa lokaci guda suka kurma uban ihu sakamakon.
.
Tsananin zafi da zogin da suka ji suka rikito kasa a matukar galabaice suka kurawa juna idanu sa adda suka fara kakarin mutuwa bisa mamaki sai sadauki murzanu yaji sadauki Ruhaisu ya bushe da dariyar farin ciki don haka sai ya dubeshi cikin matukar karfin hali ya budi baki da kyar yace yakai makiyi abokin gaba tayaya aka yi kai da zaka mutu amma kake yin dariyar murna, koda jin wannan batu sai sadauki ruhaisu ya yi kakin jini ya tofar sannan shima ya budi baki da kyar yace ina farin ciki ne zan mutu bayan na cika burina na yiwa takobina wanka da jininku yanzu ne yan uwana da kuka kashe zasuyi barci mai dadi a cikin kabarurrukansu kuma idan naje na riskesu zasu yi alfahari dani kai fa da wani farin ciki zaka mutu ? Shin zakayi alfahari ne da cewa ka mutu dan bautar sarki shardas wanda ya maishe daku karnukan farautarsa ko kuwa ?
Me kabar wa iyalinka wanda zasu cigaba da rike kansu bayan ka mutu ?
Na sani cewa kan yiwa sarki shardas bauta saboda kana tsoronsa amma ba don kuna samun

wani abu a hannunsa ba yanzu me ce ribarka a cikin bautar sarki shardas ga shi kayi mutuwar banza idan ma shardas yazo nan yaga gawarka yawu zai tofa maka tunda baka cika aikinsa ba wannan batu sai nan take sadauki murzanu yaji yayi nadamar rayuwarsa a karon farko domin ya gane kuskurensa nan take hawayen takaici da bakin ciki ya zobo masa kawai sai ya sake dannan takobin Ruhaisu a cikinsa ya zama cikakken Gawa.....
Wow Nima AlQuyraemey A nan zan dakata sai Allah ya kaimu Gobe zakuji ni da part na karshe a cikin littafin tsatsuba Kafinnan nidinne dai AlQuyraemey

TSATSUBA
Littafi Na Tara (9)
Part D.
Marubucin Littafin
Abdul azis Sani M/Gini
Abubakar Saleh AlQuyraemey
.
Koda jin wannan batu sai nan take sadauki murzanu yaji
yayi nadamar rayuwarsa a karon farko domin ya gane
kuskurensa nan take hawayen takaici da bakin ciki ya zobo masa kawai sai
ya sake dannan takobin Ruhaisu a cikinsa ya zama cikakken
Gawa.
Shi kuwa sadauki ruhaisu yana cikin wannan hali ne
na kakarin mutuwa ya hango hailur bisa doki da a
sukwane tare da sauran tsirarun yan kabilarsu
Tun daga nesa da hailur ya hango sadauki ruhaisu
zaune a kasa dirshan ga takobi a cikinsa sai ya rusa
uban ihu cikin kwalla masa kira kuma ya fashe da
kuka yana mai karawa dokinsa kaimin gudu
Yana isowa daf dashi sai yayi turjiya ya sauko
daga kan dokin ya durkushe a gabansa sannan ya kamashi
ya rungume a kirjinsa yana mai sake fashewa da
sabon kuka cikin Karfin hali sadauki ruhaisu ya daga hannunsa
ya kama kumatun
hailur suka dubi juna kowannansu na zubar da hawaye
amma sai sadauki ruhaisu yayi murmushi a gareshi
yace yakai dan uwana bai kamata kayi mini kuka ba
tunda na mutu akan tafarkin cika burin kabilar mu
alfaharina guda daya ina so ka dauke gawata ka kaita zuwa
can asalin birninmu wanda sarki shardas ya baje ka binneta
wannan itace kadai wasiyyar da zan bari bayan
raina
koda gama fadin haka sai idanun sadauki ruhaisu
suka kafe suka daina motsi kuma gaba dayan jikinsa ya
sandare

koda ganin haka sai hailur ya sake kwarara uban ihu a
karo na biyu ya rungume gawar sadauki ruhaisu
kuma ya sake fashewa da matsanancin kuka
nan take ragowar dakarun nasa dasu shadila suka kamu
da tsananin tausayi kuma suka kama kuka
basu bar wannan waje ba sai da hailur ya sa aka je aka
dauko akwatun gawa na katako aka sa sadauki ruhaisu
a ciki aka kulle sannan suka kara gaba inda suka iske tawagar
sarki hulbasu da su yarima hulkas suna yin wata irin
tafiya ta ban Al'ajabi domin da karfin sihirin tsafi suke yinta
cikin tsananin gudu na ban al ajabi kuma wannan farar
tsuntsuwa ta sihiri ce take yi musu jagora don zuwa inda hular lamsara take..

×××××× ×××××××××××

ACAN BIRNIN askandariyya kuwa sai bayan tafiyar su yarima
hulkas da tazarar sa a bakwai sannan aka ga wata irin gagarumar iska tana saukowa kasa daga sama
wadda ta dugunzuma hankalin komai da kowa dake
birnin saboda karfinta
nan fa bishiya suka rinka karyewa suna zubewa kasa rufin gidaje ya rinka kwayewa kasa ya kama girgiza
ba komai ne ya haddasa wannan masifa ba face iskar
fuka fukan aljanin dake dauke da sarki shardas da bokansa
labarusa
sai da aljanin ya duro kasa bisa tsakiyar gidan sarautar
sarki hulbasu sannan inda ya duro din ya wawake yayi rami
mai zurfi sannan iska ta dauke
nan fa jama a suka kama guje guje da iface iface aka dimauce sosai kai kace
sama da kasa ce zata hade saboda tsananin razanar da
jama ar suka yi sakamakon ganin abubuwan uku wato
ganin wannan shirgegen Aljani da kuma sarki shardas
da bokansa Labarusa
har sarki shardas ya zare takobinsa zai nausa cikin
gidan sarautar sarki hulbasu sai boka labarusa ya
tsaidashi ya dauko madubinsa na tsafi ya nunawa sarki
shardas abin da ya faru a birnin kafin su iso
koda sarki shardas yaga yadda aka kashe gaba dayan
dakarunsa su sadauki murzanu a bayan gari da dukkan
shirin da su yarima hulkas sukayi aka gudu da matarsa
shadila sai ya kamu da tsananin bakin ciki nan take gaba

dayan jikinsa ya kama makyarkyata kamar wanda aka tsoma a cikin ruwan kankara, zuciyarsa kuwa ta kama tafarfasa
kamar zata kone bai san sa adda ya dakawa bokan nasa
labarusa tsawa ba yace tsayuwar me muke yi a nan
alhalin kana gani makyanmu sun tafi dauko hular
lamsara maza muje mu kure musu gudu mu karkashesu
cikin alamun tsananin tashin hankali da karayar zuciya
boka labarusa yace ai zuwa da wuri yafi zuwa da wurwuri
idan muka ce zamu cigaba da wannan tafiya a wannan
aljani ba zamu taba iya riskar abokan gabarmu ba
kafin su isa inda hular lamsara take, wannan dokin
sihiri da yarima hulkas yake bisa yafi wannan aljani
namu karfin gudu sau arba in dole ne mu samo wani
doki wanda zai iya cin musu, cikin zakuwa sarki
shardas ya ce
to taya zamu iya samo namu dokin da zai cimma
nasu?

Koda jin wannan tambaya sai bokan ya zauna a kasa
dirshan ya karanta wadansu dalasiman tsafi na musamman guda uku ya tofa akan tafin
hannunsa na hagu sannan ya doki kasa da
tafin hannunsa sau uku
faruwar hakan keda wuya sai kasa ta fara girgiza a gabansa
nan take ta dare sai ga wani murgujejen jan doki
ya faso daga cikinta girman wannan doki ya ninka
nasu yarima shardas sau uku
koda ganin wannan doki sai boka labarusa ya mike
tsaye zumbur cikin matukar farinciki ya shafi dokin
sannan ya dubi sarki shardas cikin murmushi yace ya shugabana
ina tabbatar maka da cewa
a cikin sa a iku kacal
wannan doki zai  iya cimma su yarima hulkas muna
riskarsu sai mu kashesu mu kwace wannan tsuntsu na
sihiri tayi mana jagora izuwa inda hular lamsara take
koda jin wannan jawabi daga bakin boka labarusa
sai sarki shardas ya daka tsalle ya haye bisa kan jan
Dokin
shi kuwa boka labarusa sai ya bace bat ya sake bayya
akan dokin kuma a gaban sarki shardas ya juyo ya dubeshi
cikin murmushi
yace to sarkin sauri saika sarrafa dokin na gani idan
zaka iya
sarki shardas ya mai dawa boka labarusa murmushi yace

ai kowa a bangarensa sarki ne inda dai batun karfi ne ko jarumtaka nine
zan jagoranceka wannan aikinka ne ba nawa ba
da jin haka sai boka labarusa ya bushe da dariya
Nima Al amin Ahmed Misau na tayasu sannan ya shafi
wuyan dokin kawai sai dokin ya zabura da karfi ya
falfala da azababben gudu na gaban kwatance da al ajabi
saboda karfin gudun dokin har tashi sama yake yana
tsallake gidaje koguna da tsaunika kuma a cikin dakika
biyar kacal ya ke shafe tafiyar sa a goma,
Hakika tsafi gaskiyar maishine in ba tsafin ba babu yadda
za a yi a sami doki mai irin wannan karfin gudun '
''

AL'AMARIN su yarima hulkas kuwa bayan sun shafe tafiyar
wata guda a cikin sa'a bakwai da karfin sihirin tsafi sai
dare ya fara riskesu a cikin wani daji don haka sai
sarki hulbasu ya bayar da shawarar a tsaya a yada zango ba tare da wata gardama ba
hailur dasu yarima hulkas suka amince, nan da nan aka
kafa tantuna sannan kuyangin sarki hulbasu suka
shirya abinci
hailur ya zauna tare da yayansa yarima hulkas da jaruma
siyama da kuma matansa shadila da zalina, shima sarki
hulbasu sai ya zauna tare da matarsa luzuraina da kuma dansa yarima barmas
suna cin abinci
ita kuwa jaruma rulaiya wacce har yanzu babu wanda ya
taba ganin fsukarta ko ya san labarinta face yarima
hulkas sai ta koma can gefe daya ta nisanta da kowa ta
zauna tana cin abincinta
ita kadai a kusa da farin dokinta na sihiri a lokacin da
dokin ke yin kiwo abinsa yana cin ciyawar kasa
koda sarki hulbasu ya hango jaruma rulaiya a can gefe
daya ita kadai sai ya dubi yarima hulkas yace me yasa
waccan abokiyar tafiyar taka har yanzu taki yarda tabude
fuskarta
mu gani kuma me yasa take gudun jama a shin ba zaka bamu labarinta yanzu ba ?
Sa adda yarima hulkas yaji wadannan tambayoyi sai yayi dan guntun murmushi
sannan yace ba don waccen bakuwar ba da tuni na
dade da shekewa barzahu ta ceci raina a baya don haka
tana bina bashi
labarinta yana da yawa gami da ban tausayi da al ajabi kuyi hakuri sai mun sami
lokaci isashshe
caraf sai hailur ya tari numfashin yarima hulkas yace
ai kuwa ni indai haka ne bai kamata ka barta ta rinka

kadaita haka ba
tashi kaje wurinta ka debe mata kewa saboda na ga alamar
cewa kamar tana cikin damuwa da tunani tunda tama
kasa cin abincin sosai
koda jin haka sai yarima hulkas ya mike tsaye cikin murna
ya tafi wajen jaruma rulaiya,
da ganin haka sai yarima barmas ya dubi jaruma siyama yace
kawata idan bazaki damu ba nima ina son nayi wata
magana mai muhimmanci tare dake
koda jin haka sai jaruma siyama ta murtuke fuskarta ta daka
masa harara amma tana hada idanu da hilairu sai ta mike
tsaye ta kama hannun yarima barmas taja shi
izuwa gefe daya suka kama hira cikin raha da nishadi
lokacin da yarima hulkas ya isa inda jaruma rulaiya ke zaune
sai ya isketa cikin tunani mai zurfi don haka sai da ya
kira sunanta sannan tasan da zuwansa, yarima hulkas ya dubeta cikin alamun
damuwa ya ce yake jarumar mata kuma sarauniyar kyawawa
me ya faru naga kinyi tagumi kina tunani mai zurfi haka
koda jin haka sai rulaiya tayi doguwar ajiyar
zuciya sannan ta dubeshi cikin alamun fargaba ta
ce
yakai hulkas kayi sani cewa tun da muka yada zango a nan
wajen naji zuciyata na bugawa da karfi ina ji a jikina
cewar akwai wani mugun abu dake shirin samunmu
lallai zamanmu anan yana da matukar hadari kasani
cewa dama ina da niyyar baka irin horon yakina a cikin wannan
tafiya tamu saboda na san cewa zai amfaneka
don haka yanzu saika mike tsaye mu fara, tana gama
fadin haka sai ta mike tsaye ta zare takobinta guda biyu
shima yarima hulkas sai ya mike tsaye ya zare tasa takobin
nan take suka ruguntsume da azababben yaki mai
tsanani
koda su sarki hulbasu suka ga jaruma rulaiya na kaiwa
yarima hulkas mugayen hare hare tana neman hallakardashi har ma ta dan yankeshi
kadan a damtsen hannunsa na hagu sai gaba dayansu
suka yunkura zasu afkawa jaruma rulaiya amma sai jaruma
siyama tayi tafi tasha
gabansu tace kada ku shiga wannan yakin domin baso take ta hallaka shi ba yaki take
koya masa
kuyi tunani mana inda kasheshi take son yi ai ba za ta
ceci rayuwarsa ba a baya ba kuma idan a yanzun take son kasheshi gaba dayanmu
babu wanda ya isa ya hanata don karfin damtsenta
da iya yakinta da kuma karfin sihirinta domin karfin

tasirin sihirin tsafinta ya ninka namu sau goma
gama fadin haka keda wuya sai suka fara ganin abin
al ajabi domin nan take suka ga yarima hulkas ya fara iya
duk irin yanayin yakinta sai gashi yana iya kare hare haren
ta kuma yana mai da martani sai da suka shafe rabin sa'a
suna bakin gumurzu har ma yarima hulkas ya sami nasarar dukan kirjin jaruma
rulaiya
ta fadi kasa cikin hanzari ya ruga gareta ya bata hannunsa
ta kama ya tasheta tsaye sannan ya
dubeta cikin damuwa yace

Ki gafarceni yake jarumai jarumai koda jin haka, sai jaruma rulaiya tayi murmushi tace
aini farinciki na yi da naga yanzu ka sami nasarar kani
kas
tabbas ka sami horon yaki irin nawa, gama fadin
hakan keda wuya sai jaruma rulaiya ta dafe kanta
ta kwalla ihu kuma ta sulale kasa sumammiya
al amarin da ya razana kowa ke nan a wajen aka rugo
izwa kanta sa adda yarima hulkas ya rungumeta a kirjinsa
cikin dimauta
cikin hanzari aka yayyafa mata ruwa nan da nan kuwa
ta farfado cikin tsananin mamaki da kaduwa yarima
hulkas ya dubeta yace menene ya sameki kikayi ihu
kika fadi kasa sumammiya alhalin kina tsaye cikin
koshin lafiya
Jaruma rulaiya tace " A duk sa adda wannan Aljani wanda
ya raineni yayi mini wahayi haka nake kasancewa
barci ne yake daukata mai nauyi shiyasa kaga kamar na suma
aljani Arwasul masadul ya sanar dani cewa abokan gabarmu
sarki shardas zasu iso nan ya riskemu a cikin sa a biyu
kacal
mai zuwa don haka ya gargadeni da mu hanzarta a
cigaba da tafiya kuma yayi mini albishir cewa zamu
iya isa kogon da hular lamsara take a cikin sa a biyun
koda jin wannan batu sai kowa ya mike tsaye zumbur
aka shiga shirin gaggawa aka kwashe komai aka
hau dawakai aka kama tsala azababben gudu a cikin
daren wannan farin tsuntsu na sihiri nayi musu jagora
a sama a cikin iska
dokin jaruma rulaiya ne akan gaba yana dauke da mutum uku
wato ita kanta jaruma
rulaiya yarima hulkas da jaruma siyama
a cikin sa a biyu cif suka iso bakin wani katon kogon

dutse wanda gaba daya bayansa sama da kasansa
a shafe yake babu alamar kofar shiga, Al amin Ahmed
Misau, kowa dake wajan sai da yayi iya kokarinsa
wajan gano inda kofar shiga take amma yarima hulkas na
dafa wani wuri a jikin dutsen sai kofa ta bude suka yi arba
da cikin kogon wanda yake da tsananin haske yadda ko allura ce ta fadi za a
iya ganinta
babu komai a cikin kogon dutsen face kayan yaki iri iri
masu tsohon tarihi na manyan sarakuna da manyan
jaruman da suka shude
nan take suka hango hular lamsara a can sama bisa kan wani dutse mai tudu
kowai sai jaruma rulaiya ta dubi yarima hulkas ta ce maza
kaje ka dauko waccen hula ta lamsara anyi tane domin kai kadai kuma kai kadai ne zaka
iya daukota a nan cikinmu
Saikuma Jarumi Al amin Ahmed Misau, Amma bari na
barshi yauko saboda naci girma hmm, koda gama
fadin hakan sai yarima hulkas ya ruga da gudu ya je ya
dauko hular lamsara yana daukowa kuwa
sai kofar gogon dutsen ta fara rufe kanta, A guje yarima ya
fito yana fitowa sai ya daga hular sama da nufin ya sanyata
a kansa amma sai yaji an doki kirjinsa
saboda karfin dukan bai san sa adda ya saki hular
lamsara tayi sama ta fada kan wani tsauni mai tsawon
gaske ta kama gangarawa a lokacin da shi kuma yai
sama izuwa kan tsaunin ya fado kasa magashiyan yana
aman jini yana daga kansa sama sai yaga sarki shardas
tsaye a kansa yana yi masa murmushin mugunta boka labarusa na tsaye bisa wani jan doki a
gefe guda
kawai sai sarki shardas ya yunkura da nufin ya ruga inda hular
lamsara take ya dauketa ya sanyata amma sai yaji an daure kafafuwansa
da hannayansa da wata tufkekiyar sarkar karfe ta sihiri
ba wani ne ya daure hannun sarki shardas ba face bokansa
boka labarusa cikin tsananin mamaki da kaduwa sarki shardas ya dubi boka
labarusa yace saboda me zaka ci amanata ka hanani
daukar hular lamsara?
Koda jin wannan batu sai boka labarusa  ya bushe da
dariyar mugunta sannan ya murtuke fuskarsa yace
dashi
tabbas sai yaune na tabbatar da cewa kai wawa ne mara basira
 kana zaton tsawon
shekarun danake yi maka bauta inayi ne saboda kaunarka
idan har ka dauki haka to kayi babban kuskure
masu iya magana sunce so sone amma san kai yafi kowanne, Aski yazo gaban goshi

domin A halin yanzu littafi ya kusan karewa, ina yi maka
bauta ne saboda zuwan wannan rana da zan mallaki
hular lamsara saboda nasan cewa idan na mallaketa tamkar
na mallaki duniyar nan ne gaba dayanta, dukkanin
sarakunan duniya sai sun dawo karkashin ikona, duk
wata dukiya ta duniya sai ta zama tawa ni kadai a bincike
na nagano cewa kaine kadai sarkin da zanjingina
dashi na tsorata dukkanin bokaye da sarakunan duniya
tunanin mallakar hular lamsara tunda an san kana
nemanta kuma kowa yana tsoronka, koda boka labarusa yazo nan a zancensa
sai sarki shardas ya kuma wani gagarumin uban ihu cikin
bakin ciki ya dubi boka labarusa yace in dai don hular
lamsara ka daureni da wannan sarkar sihiri to ina umartar
ka da ka gaggauta kwanceni domin na yaki makiyana gasu
tsaye a gabana kada su kashe ni a banza na rantse
da darajar iyayena nabar maka hular lamsara bana bukatar
ta
ni dai ka barni na tsare mutuncina da rayuwata, koda jin
wannan batu sai boka labarusa ya bushe da dariyar mugunta
lokaci guda ya murtuke fuskarsa yace haba shardas ta
yaya kake zaton cewa bera zai taba yarda yayi
zumunci da mage ? Kada ka manta cewa sama da
shekaru talatin bayanake tare da kai tun kana matashi babu
wanda ya san
halinka sama dani yaudara cin amana da rashin imani duk takenka ne
shin a rayuwarka ta duniya mata nawa ka mayar gwagware ? Shin a rayuwarka ta duniya
yayaye nawa ka mayar marayu ? Al amin Ahmed Misau
Nayi imanin cewa baka san adadinsu ba
ai dama ance rana da yawa ta barawo rana daya tak ta
mai kaya
koda gama fadin haka sai boka labarusa ya dubi sarki
hulbasu yace ga wanda ya sa ka yanka danka da hannunka
kuma yasa bakin ciki ya kashe ubanka sai ka dauki fansa akansa boka labarusa ya sake
duban  jaruma rulaiya wacce har a sannan fuskarta a rufe
take cikin bakin kyalle yace da ita ke kuma ga wanda ya
kashe ubanki ya  mallake dukiyarsa gaba daya ya janyo kika girma a inda babu
mutane sai ki dauki fansa kema  ni bani da wata alaka daku
burina kwai na mallaki duniya koda gama fadin hakan
sai boka labarusa ya tashi sama kamar tsuntsu ya dira
a can sama bisa wannan tsauni ya nufi inda hular lamsara
take koda ganin haka sai jaruma rulaiya ta dubi yarima
hulkas tace idan muka bar wancan bokan ya mallaki hular
lamsara zalunci zai  shimfida a doron kasa, muma sai mun

zama bayinsa
ni zanje na yakeshi na kawai dashi kai da jaruma siyama
da sarki hulbasu ku yiwa sarki shardas irin kisan gillar da kuke son yi ku daukar mana
fansar zaluntarmu da yayi koda gama fadin hakan sai jaruma rulaiya ta cire bakin
kyallen dake fuskarta su jaruma siyama sukayi arba da
tsananin Kyawunta
sai suka cika da tsananin mamaki kawai sai suka ga jaruma
rulaiya ta daka tsalle sama tamkar daga cikin baka aka
harbota ta dira akan wannan tsauni ta nufi inda boka
labarusa yake yarima hulkas, jaruma siyama sarki hulbasu suka tunkari inda sarki shardas yake
daure a cikin sarkar
sihiri koda yaga sun durfafo shi sai ya kama kyalkyala dariya
al amarin da yayi matukar basu mamaki  kenan sarki hulbasu
ya dubeshi yace saboda me kake dariya alhalin ka san
cewa KISAN GILLAH zamuyi maka domin mu huce takaicin
bakin cikin da ka kunsa mana, al amin Ahmed Misau
Sarki shardas yayi murmushi yace ina yin wannan dariya ne
saboda dalilai guda biyu rak !
Dalilin farko shine, ba zaku iya kasheni ba inda bana daure
cikin wannan sarkar tsafi, kunga kenan ku ba jarumai bane
nikuwa na zalunceku ne saboda nafi karfinku, babu
yadda zakuyi dani don haka zan mutu ina mai farin ciki
da alfaharin na mutu a jarumi abin tsoro, dalili na biyu
kuma da yasa nake yi muku dariya shine ko kun
kasheni yanzu kamar kun kashe maciji ne baku sare
kansa ba
saboda wannan bokan nawa boka labarusa idan ya  mallaki
hular lamsara sai yafini barna da zalunci a doron kasa kun
ga kenan a karshe kuma kuma rayuwarku zata
kasance a cikin bautarsa da takaicin zaluncinsa wata kila duk ya karkasheku
sarki shardas na gama wannan jawabi sai ya cigaba
da kyalkyala dariyarsa
Yana cikin dariyar ne sarki hulbasu ya zare takobinsa ya kafta masa
mummunan sara a kaurin kafarsa ta hagu nan take kafar
ta guntule jini yai feshi da tsartuwa sarki shardas ya kwarara uban ihu sakamakontsananin zafi
da zugin da ya
ratsa sassan jikinsa koda ganin haka sai shima yarima
hulkas ya zare tasa takobin ya sare kaurin kafar
sarki shardas ta dama wato suka mayar dashi gurgu.

A dai dai wannan lokaci ne suka jiyo karafkiyar karafa
a can saman wannan tsauni suka gane cewa azababben yaki ne aka kaure dashi tsakanin
boka labarusa da jaruma rulaiya, cikin alamun fishi

hailur ya dubi yarima hulkas yace yakai dana ka tafi
izuwa ga jaruma rulaiya wacce ta ceci rayuwarka kuma kayi
mata halarci ka ceci rayuwarta ka bar mu da wannan
tsohon azzalumin abokin gabarmu mu dauki fansa a kansa
koda jin wannan batu sai yarima hulkas ya ruga da gudu izuwa jikin tsaunin
nan ya kamashi ya fara hawa shi dai wannan tsauni
saboda tsananin tsawonsa duk abin dake kansa daga
kasa ana hangoshi dan mitsitsi tamkar kuda ne
Abinda su yarima hulkas basu sani ba shine ashe can karshen
wannan tsauni wutace take dafa dutse yana narkewa saura
kadan dutsen yayi bindiga ya fara aman ruwan wutar
lokacin da yarima hulkas ya shafe dakiku masu yawa yana hawa
kan wannan tsauni yaga ko rabin tsawon tsaunin bai
kai ba sai hankalinsa ya dugunzuma ya fara
tunanin cewa anya kuwa ma zai iya kaiwa can saman tsaunin
har ya taimaka wa jaruma rulaiya ba tare da ya gaji ba ya
subuto kasa ya hallaka.

++ ++ ++

ACAN kasan tsaunin kuwa sai su sarki hulbasu suka taru
su uku akan sarki shardas suka rinka yankar naman sassan jikinsa da kadan kadan yana ihu
da kururuwa saboda tsananin zafi da zogi da azabar da yake ji
hatta kunnuwan sarki su hulbasau daban -daban suka
yankesu sannan suka kwakule idanuwansa daya bayan
daya
A haka dai suka yi tayi masa azaba kala iri iri har rai yayi
halinsa cikin mummunan kisan gilla wato sarki shardas
ya zama Gawa !
A dai dai lokacin da su hailur suka kashe sarki shardas ne
shi kuma yarima hulkas ya isa can saman wannan dogon
tsauni da kyar da sidin goshi bayan duk jikinsa ya
kukkuje sau tara yana zamewa a saman kamar zai fado kasa amma cikin sa a sai ya sake
chafe tsaunin
hakika yarima hulkas yasha
bakar wuya wajen hawa kan wannan dogon tsauni
domin kaiwa jaruma rulaiya dauki, yana isa saman tsaunin sai yayi arba da jaruma rulaiya
da boka labarusa kwance a kasa jina jina sun yiwa junansu mugayen raunika
suna jan ciki sun nufi inda hular lamsara take wacce
ke sakale a jikin wata karamar bishiya a can karshen gabar tsaunin
A wannan lokaci ne kuma tsaunin ya fara girgiza alamar
cewa wutar da ke ci a karkashinsa na yin bindiga
a sannan ne kuma hailur da sarki hulbasu da siyama suka

hau kan tsaunin da karfin sihirin tsafi kawai sai suka hango
boka labarusa da jaruma rulaiya  sun durfafi taba
hular lamsara da hannayansu shi kuwa yarima hulkas ya ruga
garesu da gudu ai kuwa sai saman tsaunin ya dare gida
biyu jaruma rulaiya da boka labarusa suka gangara
zasu fada can kasa inda dafaffen dutsen ke ambaliya
ga wuta a cikinsa muraran
cikin tsananin sa a jaruma  rulaiya ta ruko wani dutse bata
fada can kasan tsaunin cikin wutar ba amma sai taji caraf
shima boka labarusa ya cafko kafarta nan fa nauyin boka
labarusa ya fara rinjayar jaruma rulaiya koda ganin haka
sai yarima hulkas ya samu da kyar ya daka tsalle sama ya dira
a karshen tsaunin shima ya cafo hannun jaruma rulaiya ya zamana
cewa nauyinta
dana boka labarusa ya dawo hannunsa, hailur da jaruma siyama da sarki hulbasu
kuwa
sai suka rasa yadda zasu yi su kai wa su yarima hulkas dauki
saboda tsaunin cigaba yake da daddarewa ko taku
daya suka kara hallaka zasuyi , hular lamsara dake sakale
a jikin karamar bishiya itama rawa take yi wanda ke nuna
alamar a koda yaushe itama zata iya fadawa cikin
ruwan wutar nan ta kasan tsaunin ta narke
koda hailur yaga halin da ake ciki sai ya kwallawa yarima
hulkas kira yace yakai dana ka saki hannun jaruma rulaiya
domin ka ceci rayuwarka, kuma kaje ka dauko hular lamsara
kafin ka rasata har abada
Koda jin wannan batu sai yarima hulkas ya juyo da fuskarsa
ya dubi hailur a lokacin da hawaye ya zubo masa yace
yakai abbana ka gafarceni ba zan iya zabar hular lamsara
ba na bar masoyiyata rulaiya ta hallaka saboda
tana bina bashin ceton rayuwata da tayi, nikam na zabi
soyayya akan duniya ku dauki danganar rashina
itama wancan hular ta lamsara gwara a barta ta fada
cikin wutar can ta narke hakan ne kadai zai haifar da zaman
lafiya a duniya
gama fadin haka keda wuya sai nauyin boka labarusa da
na jaruma rulaiya ya rinjayi yarima hulkas su duka
ukun suka rikito daga saman tsaunin suka
fada cikin wutar dutsen dake kasan tsaunin suka hallaka
gaba dayansu !!
Koda ganin abinda ya faru sai hailur da sarki hulbasu
da kuma siyama suka kurma uban ihu suka fashe da
matsanancin kuka na bakin ciki, yayinda nima kaina Al amin

na tayasu.

ALHAMDULILLAH!!!

A nan ne wannan labarin hikayar yazo karshe Inda marubucin
yace domin jin cigaban labarin  mu hadu a littafin DARUL DAULAT, domin jin cigaban LABARIN SARAUNIYA LARBISA,
karfa ku manta cikin labarinta muke sannan muka
tsunduma cikin kuma labarin sadauki Hulkas
wanda sai yanzu aka kammala, idan Allah ya sa littafin
darul Daulat ya fito zan siyo na zo na karas muku domin
kuji yadda wasan zai kasance, kafinnan kuma zanso
kowa da kowa ya baje kwakwalwarsa ayi muhawara akan wannan hikaya
shin Da gaske ne kai/ ke zaku iya shekawa ta sanadin masoyi ?
Nidai... Baridai naji daga gareku
Amma kafinnan nidinne Abubakar Saleh AlQuyramey nake cewa Sai Allah ya kaimu gobe zaku jini da wani Sabon Littafi wanda nasan cewa zai kayatar daku Matuka
Up Up Up Up Up
comments da likes dinku yana matukar kara mana kwarin guiwa saboda haka aci gaba da suburbudowa ehem